**KOMAI NISAN JIFA…**

**EPISODE 5**

**<u>CHARACTERS</u>**

*LARABA*

*INNA*

*EZE*

*ALHAJI BATURE*

*ASABE*

*HUSSEINI*

**EPISODE 5, SCENE 1**

**Hajiya Inna's Compound – Northern Kaduna. Early Afternoon**

| | | |
|---|---|---|
| 1. | **MUSIC:** | **<u>THEME MUSIC</u>** |
| 2. | **SFX:** | **<u>CHILDRN CALLING OUT TO THEM SELVES SHEEP BLEATING. CHICKENS. FOOTSTEPS</u>** |
| 3. | **HAJIYA INNA:** | Sannu da zuwa yata, don allah tuna min sunana ki |
| 4. | **LARABA:** | Toh Hajiya Inna, sunana Laraba, ni ce sabuwar nars din da aka turu zun asibitin nan al'umar~~.~~ |
| 5. | **HAJIYA INNA:** | E haka ne sunar da mai undwa ya fada min kenan. Kin ga tsofa tasa ban iya tuna sunan ki ba - Ki gafarche ni,yata (**LAUGHS)** |
| 6. | **LARABA:** | **(LAUGHING)** Nagode kwarai Hajiaya, kuma ai ba kit sofa ba,. |
| 7. | **HAJIYA INNA:** | Mai Anguwar ya fada min kalmia masu dadi game da ke, saboda haka bana tsammanin na yi kuskure baki wannan dakin da ba kowa. |

| | | |
|---|---|---|
| *8.* | **LARABA:** | Ina tabaattar meki da cewa baza ki yi da na sanin bani dakin nan ba. |
| ~~*9.*~~ | **HAJIYA INNA:** | Allah sa haka, toh bara in kidanya maki wadanda ke zaune anan gidan |
| *10.* | **LARABA:** | Ai ko da kin kyauta Hajiya. |
| *11.* | **HAJIYA INNA:** | Ina da tagwaye maza, Hassan da Husseini. Da kuma matan su da yayansu, suna da dakunan su, taho in nuna miki dakin da zan bakin. |
| *12.* | **SFX:** | **<u>FOOTSTEPS AND DOOR OPENING.</u>** |
| *13.* | **HAJIYA INNA:** | Wannan ne dakin, dakin na da girma kwarai, ina fatan zai yi miki . |
| *14.* | **LARABA:** | Ya min kwarai, nayi farin ciki da za ki bani dakin |
| *15.* | **HAJIYA:** | Ina fatan Mai Anguwar ya fada miki nawa nace za a biya kudin hayar dakin. |
| *16.* | **LARABA:** | Ya fada min, kuma na amince zan biya hakan |
| *17.* | **HAJIYA:** | Kuma ya fada miki cewa ina son kina biyan kudin hayar wata shida-shida, kin amince da hakan? |
| *18.* | **LARABA:** | E, Mai Anguwar ya fada min, na ma taho da kudin, in baki kudin yanzu ne? |
| *19.* | **HAJIYA:** | E, kina iya biya yanzu, idan dana Hassan ya dawo zai taimaka min wajen rubuta miki shidar biya wato riciti. |
| *20.* | **LARABA** | Hajiya Inna Nagode, (**RUSTLING OF MONEY)** Hajiya amshi ki kidaya, ina fatan daidai ne |
| *21.* | **HAJIYA:** | **(RUSTLING OF MONEY)** E kudin daidai ne. **(PAUSES)** Ehen, Mai Ungwar y ace min daga kasar Zaria kike, ina ne kauyen ku. |

22. **LARABA:** **(EVASIVE)** Amma fan a jima ban je gida ba, saboda yanayin aiki na da tafitafe dayawa aciki.

23. **HAJIYA:** Laraba, kina tafetafe? Ya yar yariya kamar ke zata same dama tayi aure? Da irin tafetafe haka, yaushe za ki yi aure?

24. **LARABA:** Ai aure nufin Allah ne, Hajiya haka ma batun nawa auren ai..

25. **HAJIYA:** Gaskiyar ki, Allah zai baki miji a lokacin bada jimawa ba, taho in nuna miki sauran wurari a cikin gidan,

26. **SFX:** **FOOTSTEPS AND DOORS OPENING AND CLOSING.**

27. **HAJIYA:** Ga bangaren mata a gidan, akwai ban daki mu anan, ga kicin domin girki, zai ishe ku da matan iyayana girki, na ga kamar kiyi shirin kin zo dakin

28. **LARABA:** E Hajiya, a shirye naki in shigo dakin, bari in je in kawo kayaki na.

29. **HAJIYA:** Yauwa, ina fatan zaki ji dadin zama anan.

30. **LARABA:** Nagode kwarai Hajia Inna.

31. **MUSIC:** **BRIDGE MUSIC.**

**EPISODE 5, SCENE 2**

32. **SFX:** **BUSY STREET SCENE. LOTS OF VEHICULAR MOVEMENT. CONDUCTORS CHANTING DIFFERENT PARTS OF KADUNA METROPOLIS CAN BE HEARD.**

33. **ALH. BATURE:** Toh, Mallam Dan Kabo, ka dauki kalkilata ka lisafa, ni bana son rudu kamar abinda ya faru chan baya

*34.* **VOICE:** **(LAUGHING)** Ah Alhaji, yanzu na gamsu da lisafin ai, komai yayi daidai

*35.* **ALH. BATURE:** Yauwa, yayi kyau ka lisafa da kanka kuma ka gamsu, baza mu same matsala lokacin da z aka aiko da kudin ba.

*36.* **VOICE:** Hakika, baza a same matsalla ba, nagoda kwarai Alhaji Bature, sai anjima.

*37.* **ALH. BATURE:** **(CALLING OUT)** Yauwa, sai anjima **(PAUSES, NORMAL VOICE)** Na'am, me ki faruwa saurayi?

*38.* **HUSSENI:** Alhaji Bature, barka da rana, suna na Husseini Ahmed, Mai Ungwa ya fada min in zo in gan ka .

*39.* **ALH. BATURE:** **(WARMLY)** E Haka ne, sanu da zuwa, ina ta jiran zuwar ka, ga wurin zama.

*40.* **SFX:** **SOUND OF CHAIR BEING DRAGGED ON THE FLOOR**

*41.* **HUSSEINI:** (**NERVOUS LAUGH)** Alhaji, Nagode da aminciwa ka ganne.

*42.* **ALH. BATURE:** Mai Unguwa, ya fada min cewa kana bukatar gani na, amma bai fada min game da me bane, menene ke faruwa Husseini?

*43.* **HUSSEINI:** (**NERVOUSLY)** Alhaji, ina son in fara kasuwancin saida shayi, ina da burin nan da jimawa amma jarin taki samuwa

*44.* **ALH. BATURE:** Toh, yay azan taimaka maka? Ataikace me kaki son in yi maka?

*45.* **HUSSEINI:** Alhaji, idan zaka iya, ina bukatar dan fili a kusa da shagon ka in gina rumfa, kuma in dinga amsar kayan daga shagon ka kafin abubuwa su kankama.

*46.* **ALH. BATURE:** Kana nufin karban kayan shayin da bashi, baya ka saida shayin ka biya kudin kenan.

*47.* **HUSSEINI:** (**NERVOUSLY)** Na'am, idan ka yarda?

*48.* **ALH. BATURE:** Kana son ka dinga biya sati sati ko kullum kullum?

*49.* **HUSSEINI:** Kafin sana'ar ta kankama, zan so indinga biya wata wata, sa anan in dawo biya sati sati.

*50.* **ALH. BATURE:** Husseini, ina son matasa masu sha'awar kasuwanci, zan baka dama kuma zan tallafa maka.

*51.* **HUSSEINI:** **(SURPRISED)**Alhamdulillah, nagode Alhaji Bature, ina ciki da murna kwarai.

*52.* **ALH. BATURE:** Shawarar nan taka ta burge ne, domin idan sana'ar ka na cin gaba tawa ma zata ci gaba tunda a wuri na zaka dinga amsar kayan. Kuma bane da fargaba wurin samun kudi na tunda rufar ka zai kasance kusa da tawa .**(LAUGHS)**

*53.* **HUSSEINI:** *(***HAPPILY)** E, babu wani fargaba kwatakwata. Wayo! Na ji dadi

*54.* **ALH. BATURE:** Toh, yaushe kake son ka soma Husseini

*55.* **HUSSEINI:** Alhaji Bature, zan so in soma gobe, idan ka yarda.. (**SMALL LAUGH)** Tunda yau ba saurar lokacin fara sana'a.

*56.* **ALH. BATURE: (LAUGHS)** Abin da nake son inji kenan, Husseini da na. na tabbata wannan zai zama harkar kasuwanci mai amfani.

*57.* **MUSIC:** **BRIDGE MUSIC**.

**EPISODE 5, SCENE 3**

**NORTHERN KADUNA. MR EZE'S CHEMIST SHOP.**

58. **SFX:** **LIGHT VEHICULAR TRAFFIC. MOTOR BIKE RIDE IN AND STOPS. FOOTSTEPS. SLIDING DOOR OPENS AND CLOSES.**
**IGBO HIGHLIFE MUSIC.**

59. **LARABA:** **(CHEERFULLY)** Ina yini Oga Eze, nice Laraba sabuwar nars din da aka turo nan al'umar.

60. **EZE:** **(WARMLY)** Oh Laraba, kin kyauta da kika ziyarci mu, ga wurin zama .

61. **SFX:** **SOUND OF CHAIR BEING DRAGGED ON THE FLOOR**

62. **LARABA:** (**SITTING DOWN)** Na gode Oga Eze, nayi tunanin inzo in gabatar da kaina domin kai ke da babbar shago magani anan al'umar

63. **EZE:** **(HAPPY)** Toh inna kokari nan nars Laraba, **(PAUSES)** In kawo miki abin sha ne?

64. **LARABA:** Aa, oga Eze, nagode

65. **EZE:** Toh ba damuwa ai, na san lokacin zai zo da zaki same lokacin shan lemu anan

66. **LARABA:** (**LAUGHING)** Hakika Oga Eze **(SERIOUS)** Toh, menene kaki ganin shine babbar matsalar ta bangaren lafiya anan al'umar?

67. **EZE:** **(CLEARING HIS THROAT)** Kin dai san nib a likita bani, amma tunda na jima anan sosai, babbar matsalar inna ganin zazzabin ciwon sauro ne.

68. **LARABA:** Haba? Toh yaya zamu iya aiki mu same biyan bukata anan al'umar.

69. **EZE:** **(CLEARS HIS THROAT QUITE LOUDLY)** Laraba, ki ji, jama'a basu son sayan magani da kudin su, su fi son amsar bashi, saboda son san bazan hana su ba, kinga wannan na shafar sana'a ta.

70. **LARABA:** Gaskiya, babu dadi, sai hakuri oga Eze.

71. **EZE:** Nars Laraba, daya daga cikin matsalar da nake fuskan ta kenan fa.

72. **LARABA:** Oga Eze, ina tunanin in kafa kungiya ta al'umar wanda zata kasance da dukan mai fada aji, saboda mu yi aiki tare mun inganta harkar tsarin lafiya anan al'umar.

73. **EZE:** Zai yi kyau kuwa.

74. **LARABA:** Yauwa Oga Eze, ina fatan z aka kasance daya daga cikin wadanda ke cikin kungiyar.

75. **EZE:** Hakika, zan so in kasance daya daga cikin jama'ar kungiyan

~~76.~~ **LARABA:** Toh, zan dinga gaya maka yadda abubuwa ke kasancewa, Oga Eze ka san shirin nan na Muyi Tare?

77. **EZE:** **(EXPANSIVELY)** E mana, sun ma gayace ne zuwawurin wata taron bita da suka shirya, kuma yanzu zan iya bada bayanai ma jama'a game da hanyoyin tazarar haihuwa, ina kuma saida kwayoyin maganin tazarar haihuwar, kwaroror ruba, ina kuma iya bada shawarwari ma wanda ke bukatar wasu hanyoyin tazarar haihuwan kamar IUD, da alurai da su je asibiti.

78. **LARABA:** (**EXCITED)** Ah, yayi kyau, nayi murnan jin hakan! Zaka yi amfani a kungiyar sosai kenan ai.

79. **EZE:** Ina fatan haka nars Laraba,.

80. **LARABA:** Ina fatan kungiyar zata yi fice tawuri daukaka tazarar haihuwa saboda a same raguwar macewar mata da yara lokutan haihuwa.

~~81.~~ **EZE:** Sannu da zuwa al'umar nan  nars Laraba, tabbas wannan kungiyar zata kasance mai amfani ma jama'ar al'umar nan.

82. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**EPISODE SCENE 4**

**NORTHERN KADUNA. HAJIYA INNA'S ROOM. NIGHT TIME.**

83. **SFX:** **<u>SOUND OF A KNOCK ON THE DOOR</u>**

84. **HAJIYA INNA:** **(OFF MIC, CALLING OUT)** Wanene, shigo ciki!

85. **SFX:** **<u>SOUND OF DOOR OPENING AND CLOSING</u>**

86. **SFX:** **<u>HAUSA MUSIC IS PLAYING ON THE RADIO IN THE BACKGROUND.</u>**

87. **ASABE:** Hajiya Inna, Ina yini, ina fatan ban katse miki barci ba.

88. **HAJIYA:** Ina yini Asabe, a'a ba barci nake ba, ina sauraron wannan shirin ne a radiyo

89. **SFX:** **<u>RADIO IS SWITCHED OFF (MUSIC IN THE BACKGROUND STOPS)</u>**

90. **HAJIYA:** Asabe, akwai matsala ne? Me yasa kika tsaya, kina bata rai a bakin kofa kamar kin zo kama wani

91. **ASABE:** **(UPSET)** Ba wata matsala Hajiya Inna, Kamar nars Laraba ta kauro.

92. **HAJIYA:** **(HAPPILY)** E, na ba Nars Laraba hayar daki dazu, kin san ina ta cewa zan bada hayar dakunan da ba kowa ciki

93. **ASABE:** **(SHOCKED)** Hajiya! Kina nufin kin bada daki haya wa bakuwa?

94. **HAJIYA:** **(SURPRISED)** Asabe, ai ba bakuwa yadda kike nufi bace, Mai Anguwar ya fadi kalmia masu dadi gamai da ita, hark i ma.

95. **ASABE:** Hajiya, amma ai bai isa mu ce ita mutumiyar kirki bace harma ki kawo ta cikin gidan ki, bayan ba abinda muka sani game da ita, bamu ma san mutanen ta ba.

96. **HAJIYA:** Asabe, kin bani mamaki, yadda kika yi Magana akan ta inace ai kin dauke ke ta tamkar kauwar ki.

97. **ASABE:** **(UNPACIFIED)** Hajiya Inna, bawai saboda da yi Magana masu kyau a bangaren aikin ta, shikenan ki ga kamar ina son ta acikin gidan mu ba fa

98. **HAJIYA:** Toh, me ya sa?

99. **ASABE:** Hajiya, abi daya daga ciki shine, Nars Labara bata da aure, ni ban son wanda bata da aure a cikin gidan nan. Kada ta jan hankalin mazan mu.

100. **HAJIYA:** **(CHUCKLING)** Oho, Asabe, duk wannna kishe ne kanan?

101. **ASABE:** Ne ina kula ne kawai, ba kishe na keyi ba. Kuma bai dace mu bar abinda zai jarabci mazajenmu ba.

102. **HAJIYA:** **(STILL IN A GOOD MOOD)** Wato, ki ma kina ganin kyakyawa ce kamar yadda na gani?

103. **ASABE:** Hajiya Inna ba maganan wasa na ke yi ba fa. Na yi la’akari da iyalin nan ne fa.

104. **HAJIYA:** Aa wasa keki, wannan yariyar ta baro yan’uwanta domin ta taimaka mana da jama’ar al’umar mu. Amma ke abinda kike gaya min shine in kore ta daga cikin gidan mu ba wani hujja.

105. **ASABE:** Amma hajiaya, baza ki iya chanja ra’ayin ki ka maida mata da kudin ta bane?

106. **HAJIYA:** Kin san wani abu Asabe, na soma son yariyar, kuma ina fatan in mu zauna tare da ita cikin lafiya har tsawon da za ta kasance anan gidan.

107. **ASABE:** (**MUMBLING)** Kamar, ba kya jin dadin zama da matan yayaki da jikokin. ki

108. **HAJIYA:** **(AUTHORITATIVELY)** Asabe ya isa, na bata dakin kuma bazan sauya ra’ayi na ba.

109. **ASABE:** Toh, Hajiya, ne dai inna ganin wannan shawarar ba daidai bane..

110. **MUSIC:** **<u>THEME MUSIC AND END CREDITS</u>**